UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FACTSHEET

# KOMAI GAME DA AIKI TARE DA WAƊANDA RIKICI YA SHAFA (AAP)

**KALMAR 'AIKI TARE DA WAƊANDA RIKICI YA SHAFA' (AAP) ANA AMFANI DA ITA SOSAI A CIKIN AL'UMMA MASU TAIMAKON AGAJI. GA WATA TAKARDAR BAYANI DON TAIMAKA MUKU WAJEN FAHIMTAR MAHIMMANCIN AIKI TARE DA WAƊANDA RIKICI YA SHAFA DA YADDA ZA'A AIWATAR DASHI A FILI.**



## MENENE AAP ?

- Aiki tare da waɗanda rikici ya shafa" (AAP) yana nufin alƙawuran da tsarurruka wanda hukumomin aikin agaji suka ƙafa don tabbatar cewa ana shigar da al'ummomi yadda ya dace kuma akai-akai wajen yanke shawarwari wanda yake da tasiri a rayuwar su kai tsaye.
- Aiki tare da waɗanda rikici ya shafa yana nufin amfani da iko yadda ya dace daga masu aikin agaji, tare da gudanar da shirye-shirye masu inganci wanda ya gano darajar da ƙarfin cin gashin kai na al'umma.
- A matsayin wata ƙungiyar agaji na ƙasa da ƙasa tare da aikin kariya a matsayin abu mafi mahimmanci, UNHCR sun yi alƙawarin "sa mutane a gaba da farko" da kuma ƙarfafa bisa ga kwarewar, iyawar da burin yan gudun hijira, daga wasu ƙasashe, masu kaura na cikin ƙasar da mata, maza, yan mata da yara maza mara jihar.
- UNHCR sun yi alƙawarin ɗaukan alhaki ga mutanen da sukewa aiki ta sauraro da tallafawa buƙatun su da abubuwan da suka fifita.



Tsarin AAP na UNHCR kuma an bayyana waɗannan abubuwan da aka darajanta a Ka'idar UNHCR na Shekaru, Jinsi da Bambanci da kuma ma'anar muhimman abubuwa na ɗaukan alhaki. Waɗannan sun hada da:

1. Halarta da shigar da kowa
2. Sadarwa da bayyana ayyuka
3. ra'ayoyi da bada amsa
4. koyo da sauyin ƙungiya

UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FACTSHEET

## YAUSHE KUMA MENENE DALILIN

- UNHCR na aiki tare da waɗanda rikici ya shafa daga farin wani yanayin gaggawa har sai an gano maslaha masu dorewa.
- Wannan yana buƙatar cigaba da aiki kai tsaye da al'ummomin da suke cikin damuwa a lokacin da suke hijira, don tabbatar cewa suna iya shigar yanke shawarwari masu ma'ana wanda ya shafe su.
- Tsarurrukan ɗaukan alhaki masu ƙarfi na sa gudanar da shirye-shirye mafi tasiri da inganci.
- Aiki tare da waɗanda rikici ya shafai ba wani abu bane wanda ba'a tabbatar ba ko na tarbiya: yana da tushe wajen gudanar da shirye-shirye, wanda kuma ya kamata ya bada gudunmawa kuma ya inganta shi. AAP saboda haka wani muhimmiyar ɓangaren tabbatar da inganci a duk ayyuka na wani aiki. Tsarin taimakon agaji gabadaya ya sanya kanshi ɗaukan alhaki ga mutanen da abun ya shafa.

## YAYA ZA'A AIWATAR DA WANNAN A MATAKIN FILI?

### 1. Halarta da shigar da kowa.

Mata, maza, yara maza da mata daga asali daban-daban na iya mu'amala mai ma'ana kuma ana tattauna dasu akan kariya, taimako, da maslaha.

- Tabbatar da shirye-shirye wanda suke bada damar halarta mai ma'ana a duk matakai na gudanar da aiki gabadaya (bincike, shiryawa, tsarawa, aiwatarwa, sa ido da kimantawa). Ya kamata duk rukunai jama'a a al'ummar su samu damar shirye-shiryen. Musamman, tabbatar cewa rukunai jama'a wanda za'a iya warewa, kamar marasa rinjaye, mutane masu nakasa, da mutane masu ra'ayin jima'i daban-daban da masu shaidar jinsi daban-daban.
- Tabbatar cewa duk mutanen da abun ya shafa sun samu dama iri ɗaya kuma ba tare da nuna bambanci zuwa kariya, taimako da maslaha. Ɗauki mataki ta yadda zai sa mata, maza, yan mata da maza wanda aka tilasta gudun hijira kuma mara jihar su zama masu jurewa kuma su iya dogara da kansu.
- Gano iyawar da abubuwan fifiko na duk mutanen da abun ya shafa kuma samar da shirye-shiryen kariya, taimako da maslaha wanda ya dace dasu.

## 2. Sadarwa da aiki a bayyane.

Mata, maza, yara maza da mata daga asali daban-daban a duk ayyuka na samun damar bayanai da ya dace akan lokaci, kuma na gaskiya akan (i) haƙƙoƙin su da abubuwan da suka cancanta samu, da (ii) shirye-shiryen UNHCR da abokanai aikin su.

- Karfafa sadarwa da muhawara tsakanin UNHCR, abokanai aikin su, da mutanen da abun ya shafa a muhimman matakai a lokacin gudanar da ayyuka gabadaya.
- Bada bayani da sanarwa a harsuna, tsari, da hanyoyin wanda suka dace da al'adu, kuma suna samuwa ga, duk rukunai jama'a cikin al'umma.

## 3. Ra'ayoyi da bada amsa.

Ana karɓa kuma a maida amsa ga ra'ayoyi na tsari da mara tsari daga mutanen da abun ya shafa, kuma ana ɗaukan matakin gyara inda ya dace.

- Kafawa da kuma lura da tsarurrukan karɓar ra'ayoyi masu tasiri (hadda tsokaci, shawarwari, da korafe-korafe), ta amfani da hanyoyin sadarwa daban-daban wanda ke samuwa ga duk mutanen da abun ya shafa kuma sun dace ga duk ra'ayin sirri da wanda bana sirrin ba.
- Bada kayyayaki na mutane da kuɗi don tabbatar cewa an tattara ra'ayoyi daga mutanen da abun ya shafa cikin tsari, an amince dasu, an yi nazari, an tura gaba, kuma an maida amsa ta hanya mai inganci da sirri kuma akan lokaci.
- Haɗa kai da abokanai aiki wajen gudanar da tsarurrukan karɓar ra'ayoyi da maida amsa (inda ya dace).

## 4. Koyo da sauyin ƙungiya.

Tsare-tsare, shiryawa, zaɓan abubuwan da suka fi mahimmanci, gyaran manufa, da kimantawa ana yanke shawarwari akan su akai-akai ta duba ra'ayoyin mutanen da abun ya shafa.

- Koya daga cigaba da mu'amala da al'ummomin da abun ya shafa da kuma sauya tsare-tsare da shirye-shirye bisa ga sabin ilimin da aka ƙaru dashi ta shigar da al'umma da ra'ayoyi, duk na ɗan lokaci ko kuma don gaba.
- Auna kuma inganta ɗaukan alhaki ga duk mutanen da abun ya shafa ta binciken ƙoƙarin ƙungiya akan ɗaukan alhaki.
- Hada da mutanen da abun ya shafa a matsayin abokan aiki a lokacin gudanar da ayyuka gabadaya, hadda ta bada rahoton sakamakon bincike-bincike da matakai da zai biyo su.



More tools
and tips
to communicate with the communities on the site:
cwc.westafrica.exposed